# MATSALOLIN ILIMIN BOKO NA MATA A KARAMAR HUKUMAR WUSHISHI TA JIHAR NEJA

NA

A'ISHA BELLO ABDULKADIR

LA/3782/97

SASHIN NAZARIN HARSUNAN NAJERIYA KWALEJIN ILIMI

C. O. E. MINNA

AUGUSTA 2001

# MATSALOLIN ILIMN BOKO NA MATA A KARAMAR HUKUMAR WUSHISHI TA JIHAR NEJA

NA

AISHA BELLO ABDULKADIR
LA/3782 97

SAHIN NAZARIN HARSUNAN
NAJERIYA KWALEJIN ILIMI
C.O.E. MINNA

YAHAYA MADAKI LIBRARY
SIGN. ........
DATE. ........
C.O.E. MINNA

AUGUSTA 2001

An karanta wannan bincike, an kuma amince da shi, da cewar ya cika daya daga cikin sharrudan samun takardar shaidar N.C.E a kwalejin Ilimi ta Minna.

| | |
|---|---|
| Mai duba bincike: | Shugaban sahi |
| ............................................... | ............................................... |
| Kwanan wata…………………… | Kwanan wata……………… |

# SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan aiki nawa ne zuwa ga yanni na mariganya Hassana da marigayi ya-ya Hassan wadanda suka riga mu gidan gaskiya. Allah ya ji kan su ya rahamshe su ya kuma gafarta masu, idan kuma namu ta zo, Allah ya bamu cikawa da imani Amin summa Amin.

# GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah madaukakin sarki da ya bani iko da damar kamala wannan aikin nawa cikin nasara. Haka kuma godiya ta tabbata zuwa ga Annabin SA Muhammadu manzon SA (S.A.W)

Har ila yau ina mika godiya ta zuwa ga mahaifiya ta Malama Fatimatu da Mahaifi na Mallam Abdulkadir Bello Abom (yariman Gkoji) da Allah ya hada su tare, suka kawo ni duniya suka kuma bani goyan baya a kowani bangare na karatu na musamman wajan biya min kidin makaranta, da har na kai ga kamala karatu na. Allah ya saka masu da Alheri . Amin.

Zan kuma kara mika godiya ta ta musamman zuwaa ga Yakubu Alfa yaya na kuma masoyi na da Alhaji Bashir S.S Abuja da Dr. Umar Babayi da Baba na sarkin Gboloko – Lokoja wata Alhaji Adamu Leramo da Yanni na Malama Hussaina Abdulkadir da Malama Halima Abdulkadir da Malam Abubakar Abdulkadir da Malam Hussaini Abdulkadir da Malam Usman Abdulkadir sannan kuma da Malam Ndagi Usman. Duk kannin su sun taimaka min da shawarwari lokacin karatu na da kuma gudunmawan da suka bani lokacin karatu na da na ya kamala

Bugu da kari, ina mika godiya ta zuwa ga Mallamai na Malam Aliyu Fulani da Malam Aliyu Mohammad Busa da Malama Salamatu Jibril da Malam Maina duk kan su a sashin Nazarin Harsunan Najeriya. Sai kuma sauran Malaman mu na kwalejin da wanda suka koyar mana da wadanda basu koyar mana ba kamar su Malam Abubakar da Malam Ibrahim (Chume) mun gode Allah ya saka musu da Alheri.

Sai kuma daga karshe ina mika gaisuwa ta da kuma godiya zuwa ga Malamanmu sannan kuma mai duba aiki na watu Malama Zainab Aliyu Kusharki wanda ta bani hadin kai da kuma goyan bayon ta kuma ta kaimaka min wajan ganin cewa wannan aiki nawa ya cimma nassara. Wato (Haka ta kai ga ruwa) Na gode Allah ya saka mata da Alheri, Allah ya bar zumunci Aljanna fiddausi ita ce makomin mu Amin suma Amin.

GIMBIYA A'SHA ABDULKADIR

## ABUBUWAN DAKE CIKI


| | | | |
|---|---|---|---|
| 1 | | ILIMIN BOKO | 1 |
| | a. | ILIMIN BIKO A NAJERIYA | 1 |
| | b. | ILIMIN BOKO A AREWACIN NIJERIYA | 1 |
| | c. | ILIMIN BOKON MATA | 2 |
| | d. | ILIMIN BOKO A JAHAR NEJA | 3 |

### BABI NA BIYU

| | | | |
|---|---|---|---|
| 2. | | ILIMIN 'YA MACE A JAHAR NEJA | 4 |
| | a. | ILIMIN 'YA MACE A JAHAR NEJA | 5 |
| | b | ILIMIN 'YA MACE A KARAMAR HUKUMAR WUSHISHI | 6-7 |

### BABI NA UKU

| | | | |
|---|---|---|---|
| 3 | | MATSALOLIN ILIMIN MATA | 8 |
| | a. | NA GABA DAYA | 8 |
| | b. | A JAHAR NEJA | 8 |
| | c. | A KARAMAR HUKUMAR WUSHISHI | 8-14 |

### BABI NA HUDU

| | | |
|---|---|---|
| 4. | HANYOYIN SHAWO KAN WADANNAN MATSALOLIN | 15-22 |

### BABI NA BIYA

| | | |
|---|---|---|
| 5. | SHARHI / FA'IDAR ILIMIN MATA | 23-27 |

## GABATARWA

Ilimin jagora ne ga rayuwar dan'adam ga baki daya maza da mata. Babba da yaro ilimi ya zama wajibi mune shi.

A cikin wannan littafi zamu ga cewa yana nuna mana shigowar ilimi a Najeriya da shigowar ilimin boko zuwa arewacin Najeriya da kuma ilimin mata a Neja.
Ilimin 'ya mace a Neja da kuma karamar hukumar Wushishi yana daya daga cikin abin da wannan littafi ake magana akai da amfanin ilimin 'ya mace da rashin amfanin sa.

Har ila yau, wannan littafi ya fadakar da mu matsalolin da ilimin bokon mata ke fuskan ta a cikin wannan kasa tamu Najeriya da arewacin Najeriya da jahar Neja sannan karamar hukumar Wushishi.

Haka kuma magani hanyoyin da zamu shawo kan irin wadannan matsalolin.

YAHAYA MADAKI LIBRARY
SIGN. ......
DATE.......
C.O.E. MINNA

# BABI NA DAYA

## ILININ BOKO A NAJERIYA:

Ilimin book ya samo asali ne daga hannun turawan mulkin mallaka, su ne wadan da Najeriya ta kwato yancin ta a hannun su. Har ila-yau, ilimin boko ya samu karbuwa ne a shekarar alaf dari takwas da tamanin da biyu (1882) a kudu.

Amma ilimin boko a lokacin ta soma ne da kudinci zuwa arewacin Nigeria. Sai a shekarar ta alaf dari da shidda (1960) ne ilimin boko ya fara habbaka a Najeriya. Makarantar da aka fara kirkirowa ita ce "Government Secondary School King's College" Legos, sannan saura suka biyo baya.

A cikin shekara ta alf dari tara da gomasha biyu (1912) makarantu a Nigeria suka sami nassara sosai, an samu makarantu firamare na gwamnati guda hamsin da tara (59), saura kuma. na yan mishan ne. Tun daga lokacin ne ilimin boko ya zama sananne a Nigeria, har yau ya zamana da cewa, idan baka samu ilimin boko ba, ba za a saka ka cikin gwamnati ba.

## ILIMIN BOKO A AREWACIN NAJERIYA

Ilimin boko a arewacin Nigeriya kuwa bai samu karbuwa da wuri ba, saboda basu yarda da wadanda suka kirkiro ilimin ba, balantana ilimin karan-kan sa.

Abin da yasa haka kuwa, ilimin addinin islama ce suka sani a lokacin. Sannan kuma, suna gani cewa idan suka yarda da ilimin boko, to lai-lai ne za su juya ga addinin da ba nasu ba, wato addinin (kirista) don

turawa sun zo ne da addinin su da kuma ilimin boko a hannu, don su yaudari mutane da ilimin.

Ilimin boko ya soma karbuwa ne a kasar lakwaja (Lokoja) a shekara ta alaf dari takwas da sintin da biyu 1865) da wani mutun mai suna Dr. Baikie, a Inda aka bude makaranta aka fara koyarwa da harshen Hausa da kuma Nufanci.

Sai kuma a watan satunban shekara ta alaf dari tara da tara (1909) aka soma bude makarantar yara mata (Elementary School) a cikin jahar Kano. An fara amfani ne da malaman jahar Kano, Katsina, Sakwato don koyar wa yara. To, da haka ne ilimin boko ya soma a arewa wanda har ya kai ga yau, ilimin boko ya zama fitatce a arewacin Nigeriya. Yau kuma zama na kowa da kowa.

## ILIMIN MATA

Ilimin mata wani babban ci gaba ne ga kowace al'umma da kuma kasa baki daya. Saboda al'umma ko kasa ba zata samu ci gaba ba, ba tare da ta ilimantar da mata ba. Masu hikima sun ce "Idan aka ilimanta da mace guda to kamar an ilimantar da kasa ne). To idan muka duba sosai za muga cewa ilimin mata wani babban jari ne ga kasa baki daya, musamman ma a gidajan mu. A inda zamu ga cewa uwa ita ce malama ta farko ga yara, idan ko ta samu ilimin boko, to fa, wannan gida ta samu kyakkyawar tushe.

Ilimin mata yana da tasiri matukar gaske don kuwa, idan mata a al'umma ko a kasa, suka zama masu ilimi to fa, za a samu ci gaba ta fanni daban-daban walau; ta harkan kasuwnci ne ko harkar al'adu ne, ko harkar ilimi ne ko harkar siyasa ne, da suran makamatar su. Idan mata suka zama masu ilimi, to dole ne a samu wadannan abubuwan ci gaban. Sannan kuma dole ne kasar nan ta zama fitactciya a cikin sauran kasashe.

## ILIMIN BOKO A JAHAR NEJA

Ilimin boko a wannan jahar, kunshe take da tarihin turawar mulkin kai Ilimi. Ya soma karbuwa ne tun a lokacin da aka raba Neja daga sashin sakkwato. Wato ke nan, tun daga lokacin da ta zama jahar Neja ilimin boko ya fara bunkasa.

A yanzu kuwa, ilimin boko ya cimma nasaran gaske saboda idan mutun ya duba zai ga lungu-lungu, sako-sako, Birni da kauye a kwai makarantu da dama. To, amma kuwa, akwai, wadanda suke cikin jeji ba su da makarantu. Munufa ta na cewa ilimin boko ya samu nasarar gaske kuwa shi ne, idan mutun ya duba zai ga cewa, maza da mata, babba da yaro, iyaye mata, yara mata da dai sauran al'umma mutane sai zuwa makaranta suke yi. A nan sai muce ilimin boko ya samu karbuwa a wannan jahar, musamman ma a wannan zamani da muke ciki.

## BABI NA BIYU:

Ilimin wani sunadari ne na rayuwa wanda dan'adam ke bukata don sani ko kara sanin kansa da kansa ko al'umma kai har ma da duk lamarin rayuwa.

Ilimin'ya mace kamar yanda tarihi ya nuna ya samo asali ne a tun lokacin shigowar addinin musulunci, wanda sheikh Uthman Dan Fodio ya yi jihadi akai. Sannan kuma ya nemi da a ilimantar da ya'ya mata musulmai, ba maza kawai ba. Hakanan yar sa Nana Asama'u ta amshi hannun uban ta, ta fadakar da matan musulimai kan addinin muslunci. To, ke nan ilimin 'ya mace ya samo asali ne tun lokacin shigowar addinin musulunci ba lokacin shigowar ilimin boko ba.

## ILIMIN 'YA MACE A JAHAR NEJA

Ilimin wani muhimin abu ne ga rayuwar dan'adam, musamman ma ga 'ya mace, a cikin wannan kasa tamu da kuma jahar Neja. Domin kuwa, idan muka dubi ilimin 'ya mace a jahar Neja, mutun zai san cewa lai-lai ne ya samu amsuwa ga al'umma jahar saboda, idn muka dubi ilimi a da, da kuma yanzu, zamuga cewa akwai ci gaba sosai saboda, ilimin boko a jahar Neja ya zama abin gasa a tsakanin maza da mata.

Idan muka yi la'akari da ilimin boko a shekarun baya, za muga cewa mufi yawan dalibai da suka soma tun daga firamare har zuwa sakandare galibin su maza ne. Wato ke nan mata an bar su a baya. To, sai kuma da tafiya tayi tafiya, sai ga shi yawan mata ya zo kusan dai-dai da na maza a ko wani makarantu, har ma da jami'oi ko kwaleji ilimi.

Ilimin boko ga 'ya 'ya matan jahar Neja ya yi tasiri kwarai da gaske domin kuwa, babu wani tseraya a tsakanin su da mazaje, saboda nuna hazakar da suka yo ta faenin ilimin boko kada a bar su a baya.

Ilimin boko dangane da 'ya mace a jahar Neja ya inganta kwarai da gaske domin kuwa, abin da ya sama birni da kauyen wannan jahar, gwamnati ta gin-gina makarantu da dama, abin da ya kama kamar su:- Makarantar maza da mata na jeka -ka -dawo da kuma na kwana. Sannan uwa-uba makarantar mata zalla, akwai na jeka-ka-dawo da kuma na kwana. Kai hatta ma makarantar kimiya da fasaha na mata akwai a jahar Neja.

Idan aka yi maganar ilimi mussamma ma na boko, lai-lai ya cimma nassara kwarai , don kuwa al'ummar jahar sun karbeta hannu bib-biyu, shi yasa Gwamnati ta samu karfin gwiwa gina makarantun mata da dama wadanda suka hada da: Makarantar Kimiya da fasaha na 'yan mata.

Wanda akafi sani da (Maryam Babangida Science College Minna) Makarantar Kwalejin mata dake Bida. Wato Government Girls College Bida) Makarantar Sakandaren mata dake Minna (Government Girls Secondary School Minna)

Makarantar Sakandaren mata dake Tagina. Wato Government Girls Secondary School Tegina) Makarantar Sakandaren mata dake kafin koro wato (Government Girls Secondary School Kafin koro) da dai sauran makamantan su. Don suna nan da dama in dai makarantun mata ne a wannan jahar.

## ILIMIN 'YA MACE A KARAMAR HUKUMAR: WUSHISHI

A baya, nace ilimin boko ya samu karbuwa a jahar Neja birni da kauye, to, amma kuwa a kwai wasu kauyaku da ilimin boko bai yi tasiri sosai ba. Ko kuma muce , bai samu karbuwa sosai ba. Daya daga cikin ire-iren kauyakun kuwa ita ce karamar hukumar Wushishi.

Ilimin boko a cikin wannan karamar hukuma, bai samu karbuwa sosai ga 'ya 'ya matan wannan yanki ba. Haka ya faru ne a saboda yawancin iyayen yaran ba su da ilimin boko, sannan kuma, ba su san muhimmacin ilimin boko ga 'ya mace ba, su a nasu ganin wai, saboda fadar nan ta mutane cewar darajar 'ya mace gidan mijin ta. Ya kuma zama dole mijin nan ya biya mata duk wani bukatun ta. Shi yasa suke ganin, bai kamata su tsaya suna bata wa kan su lokaci ba wajan ilimintar da ya'yan su mata ba tun da haka ne.

Matanan wannan gari kusan duk kan su musulmai ne, kuma suna ganin cewa sun sabawa addinin su, idan 'ya mace ta kai munzulin yin aure ba a auran da ita ba kamar yadda addinin musulinci ya umurta ba. Shi yasa barin 'ya mace a wannan yanki ta kai wani lokaci ta na karatun boko bai zama al'adar su ba. Sai dai, 'ya mace iyayen ta su kokar ta su sata a makarantar firamare, in yayi tsanani zuwa kwaleji.

To, amma fa, ba ma duka iyaye ke barin yaran su mata su gama makarantar kwalejin ba. Sai kaga yarinya ta kai aji uku ko hudu a kwaleji an fitar da ita an yi mata aure wanda turawa ke cewa (withdraw) Iyayen da za a ga sun bar 'ya yan su mata sun gama kwaleji ko suna makarantar gaba da sakandare ko wata jami'a za aga cewa iyayen suma suna da ilimin boko ko da kadan ne. So suwa, wadanda Allah ya taimaka wa sai su fara karatun su, su kuma ci gaba, da tare da samun wata miskila ba har Allah ya sa su gama.

Wani dalilin da yasa ilimin boko kasance ana yi masa rikon sakainar kashi a cikin wannan karamar hukumar shi ne, su dai 'yan wannan gari mutane ne masu mu'aminla da junan su ta harkar zuman takewa. Iyayen wannan yanki ba su bada cikakken goyan bayan su ba, wajan ba wa 'ya'yan su mata ilimin boko har na wani tsawon lokaci ba, don gudun kada 'yar su ta jawo masu abin kunya a gari.Ko kuma yarinya ta shiga shashanci a gari ko a makarantanta. Dalilin yin haka kuwa shi ne don kare mutuncin su a idon jama'a da kuma, mutanen anguwa.

To amma, da tafiya tayi tafiya, yanzu iyayen ko wace al'ummar wannan gari sun fara sani da kuma fahimtar muhimmancin ilimin boko ga 'ya'yan su mata.

Wannan ya faru ne a saboda Gwamnati na kokarin wayantar da kan su wajan sanin muhimmancin ilimin ga 'ya mace a cikin al'umma da kuma cikin gidajan mu. Gwamnati ta fara fadakarwa ne ta hanyar nuna wasanin kwaikwayo a gidajan sadarwa kamar su: Talabijin da redio wajan nuna amfanin ilimin boko ga 'ya mace, da kuma ilar da ke cikin rashin ilimintar da ita. Sai kuma daga karshe, Gwamnatin jahar ta shawarci iyaye da su dai na kin sa 'ya 'yan su mata a makaranta. Sunnan kuma, idan sun sasu, da su dai na fitar da su, ya kamata su rinka barin su har sai in sun gama. Sannan kuma wanda hukuma ta kama da laifin fitar da 'ya mace daga makaranta, Gwamnati za ta hukun ta shi.

To, yin haka ya sa iyaye sun fara barin ya'yan su mata da sai sun gama makarantar su kafin a aura da su. Sannan dalilin fadakarwar da Gwamnati ta dinga yi, ya sa iyaye yanzu sun fara barin 'ya'yan su mata da su ci gaba da karatun su na 'ya'yan su mata da su ci gaba da karatun su na boko da kuma kara basu goyan baya ta hanyar basu duk wani abu da ake bukata daga makaranta. Da kuma kara basu shawara, da su kara hinma a karatun su don su samu zuwa gaba.

## BABI NA UKU

### MATSALOLIN ILIMIN BOKO NA GABA DAY

Kamar yanda muka sani cewa rayuwa tana tattare da matsaloli iri dabab daban, to haka ne ma ilimi yake tattare da matsaloli. Matsalolin dake addabar ilimi baki daya kuwa sun hada da: Yajin aiki, Harkar kudi, kudin tsarin ilimin kasa, Aiwatar da tsarin ilimin, da kuma faraucin habaka ilimin. Duk irin wadannam matsololi suke jawo koma bayan ilimi a cikin wannan kasa tamu ta taraiya.

### MATSALOLIN ILIMIN MATA A JAHAR NEJA

Tun da har aka samu matsaloli daga kwamnatin taraiya, to, babu abin da zai hana samu matsalolin a jahohi. Abin da ya kama arewaci, kudanci, yammaci babu inda ba wadannan irin matsaloli ballantana uwa-uba jahar Neja. Irin wadannan matsaloli kuwa sun hada da:
Matsalar karancin kwararrun mallamai, matsalar isassun kudi, kin sa yara makaranta musamman ma yara mata, yajin aikin mallamai, kin biyan mallamai hakin su, rashin isassun kujerun yara a aji.
Wadannan ire-iren matsaloli suna jawo muskila ga ilimin boko a jahuhi musamman ma a jahar Neja ballantana ma ace ilimin mata.

### MATSALOLIN ILIMIN MATA A KARAMAR HUKUMAR WSHISHI

Kamar dai yanda muka sani ne sha'anin matsalolin da ke tattare da ilimi a yau ya zama ruwan dare, ba ko shakka. A karamar hukumar Wushishi, ire-iren wadannan matsalolin ilimin mata bata sake zaure ba.

Watau abi duk daya ne, a wani fanning ma har sun sha kan na sauran wurare, Irin wadannan matsalolin kuwa su hada da:-

i. ADDINI:

Wannan matsala ne dake damun ilimin boko musamman ma ilimin mata. Ko wani bil-adama yana da addinin da yake bauta ma, ya kuma zama dule ga ko wani mutun ya bi dolokin addinin sa. Yayi abin da addinin sa ya umurce shi da yayi, ya kuma guji abin da addinin sa ya hana shi da aikatawa.

Saboda hakane al'umar wannam yanki basu dauki ilimin bokon 'ya mace da wani muhimmanci ba. Addinin mutanen wannan yanki shi ne addinin musulinci, saboda galinin wadannan mutane Hausawa ne kuma musulmai.

Tun da addinin musulunci bai yarda da 'ya mace ta kai wani lokaci a gidan iyayen ta ba'a yi mata aure ba, shi yasa iyayen wannan yanki basu ba da himma sosai ba ga ilimin bokon yaran su zukatan su, kuma addinin bai yarda yarinya ta kai munzulin yin aure ba'ayi mata ba, shi yasa suma basu goyi bayan yin hakan ba, sai dai su aurad da su.

To, wannan dalilin ne ilimin bokon matan wannan yanki bai samu karbuwa haka ba. Saboda haka, idan ana maganar karbuwa haka ba. Saboda haka idan ana maganar matsalolin ilimin mata, to addinni na ciki musamman ma addinin musulinci.

## AUREN WUR-WURI:

To, wannan dalilin ne ilimin bokon matan wannan yanki bai samu karbuwa haka ba. Saboda haka idan ana maganar matsalolin ilimin mata, da wur-wuri na daya daga cikin matsalolin da ilimin mata ke fuskanta. Su dai mutanan wannan yanki, kusan dukkannin su musulmai ne. Tun da musullunci yana kyamar yarinya ta kai munzulin yin aure a kin yi mat. To, shi yasa suma ko da sun sa yaran su mata a makarantar bokon, da sun fara makarantar ko sun gama ko basu gama ba. Ko ta ballaga ko bata ballaga ba, za a aurad da ita.

Aurad da yara mata da wuri baya basu damar yin karatu, wata yarinya ma tana aji uku ko hudu na firamare ko sakandare ne za a cire ta don yi mata aure. To, amma, ya danganta ne da yanda ta taso. Idan dai yarinya ta gama firamare to fa, ba za ta gama sakandare ba ballantana ta ci gaba zuwa jami'a ba. Idan ko aka aurad da ita to babu maganar makarantanta kuma.

A kwai yara mata dayawa wadanda suke son suga sun samu ilimin boko ishasshe don karuwan su da ci gaban yankin su, da jahar su, da kuma uwa-uba kasar baki daya. Wannan irin karuwa da yara mata za su samu ta hanyar ilimin boko ya hada ne da gyara dabi'un su ko hali daga munnana zuwa kyawawa. Ta hanyar gyara irin wannan halaye na su ne, zai sa su kasance 'ya'ye ne gari masu tarbiya da ladabi da biyayya a cikin al'umma da kuma sanin ya kamata. Ta irin wannan hanya ce zai kara sa su zama mata na gari sannan kuma, ko da sun zama iyaye ko nace ma idan sunyi aure, za su samu wannan ilimin da zai taimaka masu ta hanyar kula da mazajan su da kyawu da kuma mayaran su, ta hanyar basu tarbiya na gari da kuma lura dasu don rayuwar su ta inganta. Kamar yi masu wanka, dafa masu abinci da kyawu, shirya su zuwa makaranta da dai sauran ire-iren wadannan abubuwan yau-da kullun.

## Ii AUREN WUR-WURI:

To, wannan dalilin ne ilimin bokon matan wannan yanki bai samu karbuwa haka ba. Saboda haka idan ana maganar matsalolin ilimin mata, da wur-wuri na daya daga cikin matsalolin da ilimin mata ke fuskanta. Su dai mutanan wannan yanki, kusan dukkannin su musulmai ne. Tun da musullunci yana kyamar yarinya ta kai munzulin yin aure a kin yi mat. To, shi yasa suma ko da sun sa yaran su mata a makarantar bokon, da sun fara makarantar ko sun gama ko basu gama ba. Ko ta ballaga ko bata ballaga ba, za a aurad da ita.

Aurad da yara mata da wuri baya basu damar yin karatu, wata yarinya ma tana aji uku ko hudu na firamare ko sakandare ne za a cire ta don yi mata aure. To, amma, ya danganta ne da yanda ta taso. Idan dai yarinya ta gama firamare to fa, ba za ta gama sakandare ba ballantana ta ci gaba zuwa jami'a ba. Idan ko aka aurad da ita to babu maganar makarantanta kuma.

A kwai yara mata dayawa wadanda suke son suga sun samu ilimin boko ishasshe don karuwan su da ci gaban yankin su, da jahar su, da kuma uwa-uba kasar baki daya. Wannan irin karuwa da yara mata za su samu ta hanyar ilimin boko ya hada ne da gyara dabi'un su ko hali daga munnana zuwa kyawawa. Ta hanyar gyara irin wannan halaye na su ne, zai sa su kasance 'ya'ye ne gari masu tarbiya da ladabi da biyayya a cikin al'umma da kuma sanin ya kamata. Ta irin wannan hanya ce zai kara sa su zama mata na gari sannan kuma, ko da sun zama iyaye ko nace ma su zama mata na gari sannan kuma, ko da sun zama iyaye ko nace ma idan sunyi aure, za su samu wannan ilimin da zai taimaka masu ta hanyar kula da mazajan su da kyawu da kuma mayaran su, ta hanyar basu tarbiya na gari da kuma lura dasu don rayuwar su ta inganta. Kamar yi masu wanka, dafa masu abinci da kyawu, shirya su zuwa makaranta da dai sauran ire-iren wadannan abubuwan yau-da kullun.

Idan aka yi maganar cigaban jahar, za aga cewa idan mata suka samu ilimin boko a kowani karamar hukuma musamman ma a wannan karamar hukumar Wushishi, to dole ne a samu ci gaba a wannan yanki. Idan wannan yanki ya kasance yana da ilimantattun yara musamman ma yara mata, to dole ne ma wannan jaha ita ma ta samu ce gaba. Wannam irin ci gaba kuwa, zai iya kasancewa:-

Za a samu yara mata masu hazaka da ilimi wanda ma jahar zata yi alfahari da su har ma Gwamnatin jahar ta tura su zuwa karo ilimi a ko-ina, kai har ma da kasar waje ta hanyar daukar nauyin su, don karowa kan su da kuma jahar su don ci gaban kan su da kuma jahar su.

Ta hanyar samun ilimintattun mata ne a cikin jaha yakan sa kaga an samu Darakta ko kwamishina ko wasu ingantattun mikami a cikin jaha wandanda suke mata ke rike da irin wadannan mukamumi.

Idan kuma aka yi maganar gudun mawar da mata za su iya bayarwa a cikin kasa idan dai har suka samu ilimi ingantatce sai muce yana da dama. Don kuwa, idan muka duba, za muga cewa babu irin mukamin da namiji zai iya rikewa da ita ma mace ba za ta iya rikewa ba idan dai har tana da ilimin ta, don ci gaban kasar ta.

Irin wannan ci gaba kuwa da mace zata iya bayarwa idan har tana da ilimin boko sun hada da:-

Mace zata iya rike mikamin minsta ko Darakta ko mai bawa shugaban kasa shawara a fannoni daba-daban ko zama shugaban mata na kasa baki daya ko Darakta-janar da dai sauran su. Za mu yi misalai da irin wadannan mata dake rike irin wadannan mikami kamar su:- Hajiya Aisha Isma'il Minista ce mai kula da harkokin mata da cigaban matasa na kasa, Da Mrs Kaina Chukwelu Minista ce mai kula da sufurin jiragen sama da sauran su.

A kwai kuma wasu yaran da suke da burin so suga sun zama wani abu a rayuwar su kamar su zama Nurse ko lauyaji ko mammaman

makaranta da dai sauran su. To, yanda iyayen su suke karye masu kwaiwu dangane da ilimin su ta hanyar aurad da su da wur-wuri, ya janye masu rashin cimma burin su na rayuwa.

## Iii BATA MARTABAR IYAYE A IDON JAMA'A

YAHAYA MATA... LIBRARY SIGN. DAT... C.O.E.

Wannan ma wani dalili ne dake wargazar da aniyar ilimin boko 'ya mace a wannan yanki don kuwa, iyaye da dama suna jin tsoron sa yaran su mata a makarantar boko musamman ma a cikin wannan yanki don gudun la-lacewa.

Iyaye na ganin cewa, tura yaran su mata ne zuwa makarantar boko ke kawo lalacewar ta ta hanyoyi da dama soboda dama tun chan ilimin boko na da wannan tabon musamman ma ga iyayen arewa cewa: mudin yara suka samu ilimin boko, to fa hanyar lalacewa ya zo kenan musamman ga mata" Wannan irin shashanci da iyaye ke kirari kuwa sun hada da:

Rashin jin maganar iyaye, bin lalattun abokai, ratsewa wani wuri bayan an tashi makaranta kamar: Ziyartar saurayi ko wani wurin da iyayen su ba sason suje, da dai sauran ire-iren su. Irin wadannan dabi'u kan janyo lalacewar yara mata har ya kai ga sun dauko wa iyayen su abin kunya a gari, ko muce abin fadi wato, yin ciki ba tare da anyi aure ba.

## Iv TSADAR KAYAYYAKIN KARATU

Wannan dalili yana sawo na nashi gudunmawa wajan tabarbarewar ilimin boko musamman ma na mata a cikin wannan yanki.

A kwai iyayen da suke da yara fiye da uku ga shi kuma ba su da isasshen wadata ga kuma kayan karatun yara sun yi tsada. Irin wannan yanayi shi ke jawo iyaye su ki sa yaran su mata a makaranta boko, sai

kaga sun fi sa himma wajan sa yaran su maza a makaranta sai su bar mata a gida. Idan kuma sun bar su da su yi karatun, to da kyar ne yara matan ke gamawa musamman ma idan sun kai ajin karshe inda za a bukaci iyaye da su biya dubbai wajan biyan kudin jarabawar yara ne karshe wata (S.S.C.E.)

Wannan irin kudi ba duka iyaye za su iya biyan wannan irin kudi ma yaran su ba ballantana iyayen da suke da yara fiya da biyu ko uku wadanda za su zauna wa wannan jarabawa.

To, a irin wannan lokaci ne iyaye kan fake don kire yaran su mata daga makaranta da cewa basu da kudin biya masu sai su bar su zabe yaran su maza su biya masu sai su bar dukkan su. Sai su zabe yaran su maza su biya masu sai su bar mata. Irin haka na jawo matsala ga ilimi musamman ma na mata a cikin wannan yanki.

## v. RASHIN ISASSHAN ILIMIN BOKO GA IYAYEN:

Iyayen wannan yanki da daman su basu da ilimin boko. Shi ya jawo rashin sanin muhimmancin ilimin wanda yasa ake samun matsala wajan sa yara makaranta musamman yara matan wannan yanki. Dole ne iyaye ke da alhakin sa yaran su makaranta, sai gashi an wayi gari iyayen dake da wannan alhaki basu san muhammancin sa ba, ballantana su tura yaran su mata don samun wanan ilimin

Wannan rashin sanin muhimmancin ilimin ya dauko ashali ne a inda iyayen wannan yanki galibin su jahilai ne ga ilimin boko saboda, sun fi ba ilimin mahammadiya karfi saboda shi suka sani ilimi tun zamani iyaye da kakanni wanda iyayan su suka nuna manu ke nan suka kuma tura su don sanan addinin su so-sai. To, shi yasa ake yiwa ilimin boko rikon sakainar kashi a wannan yanki.

Tun da iyayen basu san muhimmancin wannan ilimin ba sai suka ki sa himma wajan tura yaran su mata makarantar bokon, sai dai na mahammadiya. Wannan dalilin ya kawo tabarbarawar ilimin boko yara mata a cikin wannan yanki.

## BABI NA HUDU

## HANYOYIN SHAWO KAN WADANNAN MATSALOLIN

A kwai hanyoyi da dama da za a iya bi domin shawo kan matsalolin dake addaban ilimin mata a cikin wannan kasa tamu Nigeriya, musamman a wannan yankin na jahar Neja.

Kafin na je ga hanyoyin da za a iya bi domin shawo kan wadannan matsaloli, ya cancanta na tabu dan kokarin da Gwamnatin Nageriya ta fara yi don kawo karshen irin wadannan matsalolin.

Da farko dai Gwamnatin Najeriya ta fara ne da bayyanar da kasidu a kan ilimin mata da kuma muhimmancin sa a tarun da aka yi na kundin tsarin ilimi na kasa wanda aka shirya a alof dari tara da sittin da tara (1969).

To, wannan taru bai samu cimma burin sa ba sosai, sai a tarun hadin kan kasashe da aka yi ne wato (U.N.) na alaf dari tara da saba'in da biyar zuwa alaf dari tara da tamanin da biyar (1975 - 1985) ne aka kara karfafa maganar ilimin mata da kuma tazaran dake akwai a tsakanin ilimin maza da mata sosai da sosai. Sannan kuma Gwamnatocin kasashe wanda ya hada har da Najeriya suka kara nuna damuwar su akan ilimin mata da cewa:-

"Idan dai har ana son kowace kasa ta samu ci gaba, to dole ne Gwamnatin kasar ta kara himmatuwa wajan ilimintar da mata musamman a fannoni kamar hanyoyin kara inganta sana'oi da kiwon lafiya da dai sauran su".

Har ila yau, Gwamnati Najeriya ta kara nuna damuwar ta a kan nunin wariya da ake yi wa mata a bangaren ilimi. Don haka ne Gwanmati ta faddamar da hukumar ilimi na mata a kasar nan. Ita wannan hukuma ke

kara nuna wa jama'a ma'anar dedantakar dake tsakanin ilimin maza da na mata, da kuma hanyoyin da za a bi don cimma kassara.

Idan ana son ilimin mata ya ci gaba da kuma cimma burin sa, to dole ne sai an samu chanjin halaye na gari dangane da ilimin mata ta kowace hanya ko kuma Gwamnati ta kafa doka kamar:-

i. HANA FITAR DA YARA MATA DAGA MAKARANTA

Ya kamata Gwamnati ta tashi tsaye wajen kafa dokar hana iyaye fitar da yaran su mata daga makarantar boko, don wasu ko wani dalili kamar yi masu aure ko don sana'a da dai sauran dalilai. Gwamnati ta jawa iyaye kunne da cewa, duk wanda aka kama da yin hakan to, ba shakka Gwamnati zata hukunta shi. Idan ma suna son yin haka ne, sai su bari sai in ta kamala ko kuma sai ta mallaki hankalin kan ta tukunnan wato ma'ana in dai ta san ciwon kanta. To, alukacin ko da tayi auren zata so ci gaba da karantun ta. Idan har Gwamnati ta kafa irin wannan doka ga iyaye to, ba shakka za su dai na fitar da yaran su mata daga makaranta, don gudun kada Gwamnati ta hukunta su ko ta ci su tara.

Ii GIGGINA MAKARANTUN MATA DA DAMA

Ya kamata Gwamnati ta dauki halin ya kamata wajan giggina isassun makarantun mata da dama a cikin kasar nan. Sannan kuma idan an tashi gina su, ya kamat Gwamnati ta bi birni da kauye, lugu-lungu, soko-soko don kara karfafa ingancin dake a kwai na ilimintar da mata musamman yara mata zuwa makarantar boko.

Haka kuma irin wadannan makarantu ta mata, idan Gwamnati zata gina su, ya kamata ta fara tun daga Gwamnatin taraiya zuwa jaholi har ya zuwa kananan hukumomin wannan kasa don cimma cikakkiyar burin abin da ake nema.

Ire-iren wadannan makarantu na mata ya hada da makarantar yara mata ko makarantar maan aure ko makarantar yaki da jahilci na mata zalla. Giggina irin wadannan makarantu zai kara inganta ilimin mata a kasa, haka kuma zai kara sa wa iyaye ra'ayin tura yaran su mata zuwa makarantan boko. Masamman ma idan suna da wasu shakku a kan sa su don taimakawa kai da al'umma da kuma kasa ba tare da sun gwamatsu da maza a cikin aji wajan karatu ba.

i. FADAKAR DA IYAYE

Jahiki ga iyaye yana daya daga cikin abin da ke jawo koma bayan ilimin yara mata a kasar nan musamman a bangaran yara mata.

Ya kamata Gwamnati ta dauki kwararan matakai na kawo karshen rashin sanin muhimmancin ilimin mata dake addabar iyaye musamman ma a cikin karkaran mu a yau. Gwamnati za ta tashi ne haikan wajan fadakar da al'ummar kasar na, don sanin amfanin ilimin boko ga yara mata da kuma ilar dake tattare da rashin sa. Idan Gwamnati ta tashi fadakarwa, ya kamata ta tashi wajan zagayar birni da kauye don fadakar da al'umma musamman ma iyaye wadanda suke jahilai ga ilimin boko, da wadanda basu dan muhimmancin sa ga mata ba, da kuma wadanda suke masa mummunar fahimta to, ta wannan hanya ce za su iya ko su kara fahimtar amfanin ilimin boko ga yaran su mata.

A kwai hanyoyi da dama wadanda Gwamnati za ta iya bi don fadakar da al'umma da wayantar masu da kai a kan ilimin yaran su mata. Irin wadannan hanyoyin kuwa sun hada da:- Kafofin watsa labarai, kamar su:Radio da talabijin, Akwai kuma hanyar sadarwa kamar su: Jaridu, Kasidu, littattafin karatu da dai sauran su. Irin wadannan hanyoyi idan Gwamnati ta kara karfafa yin amfani da su wajan fadakar da al'umman wannan kasa to, ba shakka ilimin boko zai kara karfi da kuma amsuwa ga jama'ar kasar nan musamman ga yara matan su.

ii. ILIMI KYAUTA KO RAGE FARASHIN KAYAN KARATU

Kamar yanda muka sani ne Gwamnati na kokari wajan bada ilimin boko kyauta a cikin wannan kasa a kuma wannan zamanin. Ire-iren irin wannan ilimi kuma sune kamar su:- Ilimin yaki da jahiki, bin makyaya wato (Fulani) har ruga wajan ilimintar da su kyauta, koyar da yaran makaranta yan aji, daya zuwa aji uku kyauta da dai sauran su. Duk irin wadannan yana taimakawa ne wajan yaki da jahilci da kuma ganin ci gaba ilimi a kasa.

To, amma har ila yau Gwamnati na da saura ciki a gaban ta domin kuwa, idan har Gwamnati na so ta shawo kan irin wadannan matsaloli dake jawo barazana wajan koma bayan ilimi a wannan kasa da kuma wannan jahar. To, dole ne Gwamnati ta kara daukar kwararan matakai da zasu kara inganta ilimin bokon su kuma ya kara bawa iyaye karfin gwaiwa wajan tura yaran su makaranta musmman yara mata.

Irin wadannan karfin gwaiwa kuma da Gwamnati da ya kamata ta kara bawa iyaye kuwa sun hada da:-

Bawa yara mata ilimi kyauta, Rage kudin makaranta musamman ma ga 'yan karshe wato (S.S.C.E.) Rage farashin takardun karatu da rubutu.

In dai al'umma ko mace iyaye za su samu Karin ire-iren wadannan taimako to, dole ne a samu bunkasuwa ilimin boko a cikin kasar nan. Saboda kuwa, hatta iyayen da basu son tura yaran su makaranta za su samu karfin gwaiwar tura su. Da kuma iyayen da Allah ya albarkace su da yara da yawa kuma basu da isasshen wadatan tura su makarantar boko gabaki dayan su, sai su tura yaran su makaranta.

Saboda haka nan, ya kamata Gwamnati ta dauki irin wannan mataki don ganin ci gaban kasa da jaha da yaye jahilci a cikin kasa musamman ga mata da kuma taimakawa iyaye musamman ga mata da kuma taimakawa iyaye mussamman mara sa wadata don taimakawa kai da kai.

iii. FADAKAR DA IYAYE

Jahiki ga iyaye yana daya daga cikin abin da ke jawo koma bayan ilimin yara mata a kasar nan musamman a bangaran yara mata.

Ya kamata Gwamnati ta dauki kwaranan matakai na kawo karshen rashin sanin muhimmancin ilimin mata dake addabar iyaye musamman ma a cikin karkaran mu a yau. Gwamnati za ta tashi ne haikan wajen fadakr da al'ummarkasar na, don sanin amfanin ilimin book ga yara mata da kuma ilar dake tattare da rashin sa.

Idan Gwamnati ta tashi fadakarwa, ya kanata ta tashi wajan zagayar birni da kauye don fadakar da al'umma musamman ma iyaye wadanda suke jahalai ga ilimin book da wadanda basu da muhimmancin sa ga mata ba, da kuma wadanda suke masa mummanar fahimta to, ta wannan hanya ce za su iya ko su kara fahimtar amfanin ilimin boko ga yaran su mata.

A kwai hanyoyi da dama wadanda Gwamnati za ta iya bi don fadakar da al'umma da wayantar masu da kai a kan ilimin yaran su mata. Irin wadannan hanyoyin kuwa sun hada da:-

Kafofin watsa labarai, kamar su: Radio da talabijin. Akwai kuma hanyar sadarwa kamar su: Jaridu, Kasidu, limattafin karatu da dai sauran su. Irin wadannan hanyoyi idan Gwamnati ta kara karfafa yin amfani da su wajan fadakar da al'umman wannan kasa to ba shakka ilimin book zai kara karfi da kuma amsuwa ga jama'ar kasar nan musamman ga yara matan su.

iv. ILIMI KYAUTA KO RAGE FARASHI KAYAN KARAKU

Kamar yanda muka sani ne Gwamnati na kokari wajan bada ilimin book kyauta a cikin wannan kasa a kuma wannan zamanin.

Iri-iren irin wannan ilimin kuma sune kamar su: Ilimin yaki da jahilci, bin makyaya wato (Fulani) har ruga wajan ilimintar da su kyauta, koyar da yaran makarnta yan aji, daya zuwa aji uku kyauta da dai sauran su. Duk irin wadannan yana taimakawa ne wajan yaki da jahilci da kuma ganin ci aban ilim a kasa.

To, amma har ila yau Gwamnati na da saura aiki a gaban ta domin kuwa, idan har Gwamnati na so ta shawo kan irin wadannan matsaloli dake jawo barazana wajan koma bayan ilimi a wannan kasa da kuma wannan jahar, To, dole ne Gwamnati ta kara daukar kwararran matakai da zasu kara ingantta ilimin boko su kuma kara bawa iyaye karfin gwaiwa wajan tura yaran su makaranta masamman yara mata.

Irin wadannan karfin gwaiwa kuma da Gwamnati za ta ba wa iyaye kuw sun hada da:-

Bawa yara mata ilimi kyauta , Rage kudin makaranta musamman ma ga 'yan karshe wato (S.S,C.E.) Rage farashin takardun karatu da rubutu.

In dai al'umma ko mace iyaye za su samu Karin ireiren wadannan taimako to, dole ne a samu bunkasuwa ilimin boko a cikin kasar nan. Saboda kuwa, hatta iyayen da basu son tura yaran su makaranta za su samu karfin gwaiwar tura su. Da kuma iyaye da Allah ya albarkace su da yara da yawa kuma basu da isasshen wadatan tura su makarantar boko gabaki dayan su, sai su tura yaran su makaranta.

Saboda haka nan, ya kamata Gwamnati ta dauki irin wannan mataki don ganin ce gaban kasa da jaha da yaye jahilci a cikin kasa musamman ga mata taimakawa iyaye mussamman mara sa wadata don taimakawa kai da kai.

## V. GUJI TURA YARANSU MATA ZUWA WASU SANA'OI

A kwai Al'adu da dama da jamar kasar nan suka dauka ta wadannan al'adu basu goyan bayan ilimin mata. To, kamar yanda za mu gani mutane kan ce "MATA ANFANIN SU A GIDA YAKE" shi wannan tunani ko zance na mutane ba daidai bane, don kuwa, ba a yi mata don zaman gida kawai ba.

Saboda haka nan, ya kamata jama'a ko in ce iyaye su kau da wannan harsashan su san cewa ba a yi mace don zaman gida kawai ba. Kamata yayi iyaye su himmatu wajan tura yaran su makaranta don samu ilimin zamani musamman ga yara mata.

Kamar yanda iyaye kan tura yaran su mata wajan neman kudi, to tura su sana'oi irin daban - daban a mai makwan tura su

Bawa yara mata ilimi kyauta , Rage kudin makaranta musamman ma ga 'yan karshe wato (S.S,C.E.) Rage farashin takardun karatu da rubutu.

In dai al'umma ko mace iyaye za su samu Karin ireiren wadannan taimako to, dole ne a samu bunkasuwa ilimin boko a cikin kasar nan. Saboda kuwa, hatta iyayen da basu son tura yaran su makaranta za su samu karfin gwaiwar tura su. Da kuma iyaye da Allah ya albarkace su da yara da yawa kuma basu da isasshen wadatan tura su makarantar boko gabaki dayan su, sai su tura yaran su makaranta.

Saboda haka nan, ya kamata Gwamnati ta dauki irin wannan mataki don ganin ce gaban kasa da jaha da yaye jahilci a cikin kasa musamman ga mata taimakawa iyaye mussamman mara sa wadata don taimakawa kai da kai.

## V. GUJI TURA YARANSU MATA ZUWA WASU SANA'OI

A kwai Al'adu da dama da jamar kasar nan suka dauka ta wadannan al'adu basu goyan bayan ilimin mata. To, kamar yanda za mu gani mutane kan ce "MATA ANFANIN SU A GIDA YAKE" shi wannan tunani ko zance na mutane ba daidai bane, don kuwa, ba a yi mata don zaman gida kawai ba.

Saboda haka nan, ya kamata jama'a ko in ce iyaye su kau da wannan harsashan su san cewa ba a yi mace don zaman gida kawai ba. Kamata yayi iyaye su himmatu wajan tura yaran su makaranta don samu ilimin zamani musamman ga yara mata.

Kamar yanda iyaye kan tura yaran su mata wajan neman kudi, to tura su sana'oi irin daban - daban a mai makwan tura su

makarantar boko to, sam bai chanchanta ba ya kamata su dai na, don kuwa bai da amfani ga kasar mu, ga al'umma, ga gidajan mu sannan kuma uwa uba kuma ga mu kan mu.

Tallace - tallace nan a kan titi ko tura yara mata gidajan masu wadata don yin boyi-boyi ko wanke- wanke ko sharan gida ko rainon yara don su samar wa iyayen su kudi ko kuma biya wa kan su bukatu wato ke nan yaran suma su dauki nauyin kan su da kansu a mai makon iyayen su. Irin wadannan abubuwa da iyaye ke tura 'ya'yan su mata su je su yi don su kawo masu kudi a mai makon tura yaran su mata zuwa makaranta bai da alfanu ga 'ya'yan su har ma da su iyayen, ba kuma zai tsinana masu komai ba.

Saboda haka nan ina kira ga jama'a, Al'umma, iyaye da su guji yin amfani da yaran su mata wajan ire-iren wadannan sana'oi don samun kudi ko biyan bukata.

Ya kamata su sawa zuciyar su akidar turan su mata zuwa makaranta, a mai makwan azabtar da su ta irin wadannan hanyoyin rayuwa don kare mutuncin su da kuma na yaran su mata.

# BABI NA BIYAR

## SHARHI / FA'IDAR ILIMIN MATA

Ya kamata ilimin mata a kasar nan Gwamnati ta dauke shi da fa'ida ta hanyar bunkasa shi. Kamar yan da na fadi a cen baya cewa idan ana so a farfado da ilimin mata so-sai to dole ne Gwamnati ta fara kawo na to gudun mawan, ta hanyar fadakar da al'umma musamman iyaye don su kara don su kara sanin amfanin ilimin mata. Har ila yau kuma, Gwamnati ta kara fadada ilimin mata a kasar nan musamman ma a wannan karamar hukumar nan na Wushishi ta hanyar gigginan makarantun boko ta mata.

Wadannan irin makarantun ta mata zalla kuma, ya kamata Gwamnati ta faro tun daga tushi, wato daga firmamare sannan uwa-uba sakandare. To, tayin haka ne ilimin mata zai kara bunkasa sannan kuma ya kara karbuwa ga al'umma.

Bai kamata Gwamnati ta fi ba da karfi wajen giggina makarantun mata a cikin birni kawai ba. Ya kamata ta bi birni da kauye wajan gina irin wadannan makarantun don al'ummar dake birni da kuma kauye lungu da sakon wannan kasar. Gwamnati kuma kada ta tsaya ga makarantar yara mata kawai, ya kamata ta zarce har da na matan aure, ya kamata Gwamnati kada ta barsu a baya domin kuwa, a kwai wasu yara matan da suka fara makarantar boko sunnan kuma basu kare ba aka aurad da su. A kwai kuma wasu yaran da ma ba su da ilimin bokon ma sam-sam. Irin wadannan mata ya kamata Gwamnati ta gina masu irin nasu suma makaranta daban, wato makarantar matan aure. Irin wadannan makarantu ta matan aure kuwa Gwamnati ta giggina su ne birni da kauye kada ta ba wa birni fifiko kawai ga irin wannan makarantu ta matan aure.

Ta fuskar iyaye kuma a kan ilimin yaran su mata kuwa sharhin da zan yi shi ne, ya kamata iyaye su ba wa 'ya'yan su maza da mata ilimin boko daidai don muce takaici.

Bai kamata iyaye su ce ba za su tura ko sa yaran su mata zuwa makarantar book ba sai dai makarantar hamamadiya kawai wannan tunani ba daidai ba ne domin kuwa, ko Allah subuhanahu wata'ala ya ce"Kunemi ilimi a duk inda yake". To, a nan ma mungani kenan cewa, ilimin mahammadiya ba, bai kuma ce na book ba. Shi dai ya ce ilimi, saboda haka nan babu ilimin da yake banza ke nan.

Saboda haka nan, iyaye su tura yaran su mata makarantar mahammadiya don taimaka masu duniya da lahira. Haka kuma, su tura su makarantar book don shi ma zai taimaka masu a nan duniya. A bin da ya sa haka kuwa shi ne, ba kasafai ake sa jahila a kowani harka a zamanin nan da muke ciki ba. A babu-babu, ya kamata 'ya mace ta iya rubutu dakaratu saboda dalilai da dama kamar haka:-

- HUCE TAKAICI: Wato, kamar taga 'yan uwan ta mata suna rubutu, ba zata yi tataicin cewa bata iya ba
- SIRRI : Za a iya rubuta mata wani abin sirri ko wasika, to ba sai ta kai an karanta mata ba.
- ZUWA BAKON WURI. Idan mace ta iya karatu ko kuma rubutu to, babu yanda za'a yi ta je bakon wuri ta bata.

Irin wadannan dalilai na nan da dama da ya kamata mace ta samu ilimin book a kalla ma iya rubutu da karatu saboda su.

Ya kamata iyaye su sani cewa tura yaran su mata zuwa makarantar book yana da fa'ida a gare su da kuma yarana su don

kuwa, ko da sun tashi aurad da su za a matunta masu 'ya 'yan a kuma dauke su da daraja saboda ilimin nan da suka samu. Abin da ya sa haka kuwa shi ne, a zamanin nan da muke ciki yawancin maza sunfi son mace mai ilimin book ko da kuwa suma ba su da ilimin. Sannan kuwa namiji dake da ilimin, ya fi son mace mai ilimi don kuwa ba zai so ya auri mace jahila ba.

Saboda haka, ina kira ga iyaye da su dauki halin tura yaran su mata zuwa makarantar book don ko da sun tashi aurad da su za a kale su da daraja, kuma, ko daq kuma sun yi auran za a daraja su, a mutunta su, a kuma girmama su daga mijin har ya zuwa 'yan'uwan su, ballantanan ma har ya kai ga yi masa gorin rashin ilimin zamani babu haka sam-sam zuwa gare su.

Ilimin boko ga yara mata yana kai su ga daukaka a cikin al'umma, saboda idan mace tana da ilimin boko, babu wani aikin da namiji zai yi da macen nan ba zata iya ba musamman ma aikin Gwamnati kamar:-

Aikin koyarwa, aikin likita, aikin lauya, aikin hada magunguna, Tukin jirgin sama da dai sauran su.

Haka kuma, idan aka yi zance mukami, in dai 'ya mace ta yi makarantar boko, to, babu waani mukami da za a bawa namiji da ita ma baza'a iya bata ba. Mata na rike mukamai kamar su:- Minista, Darakta, sakatariya, furinsifal, kwamishina, shugaban wani sashi a manyan makarantun mu kamar jami'a ko kwalejin ilimin da dai sauran wasu manyan kamamai da za a iya samu a cikin al'umma. Duk samun ilimin boko ne ga 'ya mace zai kai ta ga irin wadannan matsayin. Saboda haka nan, duk mace mai rike da irin wadannan matsayi dole ne ta samu daraja da daukaka a cikin al'umma, kai har

ma a cikin gidan su da ma cikin 'yan'uwan ta sai kaga suna bata girma ko da itace kuwa karama.

Idan dai ilimin boko ga matan wannan kasa ta mu Najeriya ya samu bunkasa da kuma karbuwa, to, dole ne a samu karancin mata jahilai a cikin al'umman mu musamman a cikin gidajan mu. Saboda masu hikimar magana kan ce "ilimintar da 'ya mace guda kamar an ilimintar da gari guda ne"

Saboda a duk gidan da aka samu mace mai ilimin da mace jahila a bangarori da dama kamar:-

Ta janyar tarbiyantar da yara ko kula da gida ko tsabtace muhallin ko tsabtace abincin su kai hatta ma tsabtar kai dole ne a samu bambanci a cikin rayuwar wadannan gidajen biyu.

Har ila yau idan aka samu mace a gida mai ilimi dole ne a ga yaran gidan nan maza da mata an tara su makaranta do da suna so ko ba su so. Haka kuma zai tusa masu son zuwa makarantan, ba saboda komai ba sai don uwar su ke kara basu karfin gwaiwa ta hunyar tarbiyantar da su don su so ilimi. Sannan kuma za tai ta nuna masu amfanin ilimin boko da kuma ba su misalai da wadannan suka zama manyan mutane a al'umma wadanda ilimin boko ne ya kai su ga rike irin wadannan mukamai don suma suyi koyi da su dai har suna so su zama kamar su. Sannan kuma za tai kt sanun damar duba aikin da suka yi a makaranta da kuma wanda aka basu suyi a gida. Ba kuma zata dinga barin su kowani lokaci suna wasa a gida ba ta tare da suna daukar takardan su suna duba abin da aka koyar masu a makaranta ba. Sannan kuma ya kamata Gwamnati ta rin ka bawa mata dake zuwa makaranta (scollashi) wato irin kudin nan da Gwamnati ta kan bawa yaran dake manyan makarantu irin su jami'a, Gwalejin ilimi da sauran ire-iren wadannan makarantu.

Irin wannan kudi da Gwamnati ke bayarwa ga yara dake karatu a manyan makarantu, ya kama ta, ta fara bawa mata suma dake karaku kamar daga sakandare kafin ma su je ga zuwa manyan makarantu. Yin haka ga Gwamnati zai kara wa iyaye karfin gwaiwa kai hatta ma yaran dake zuwa makarantan za su kara kwazo da sa himma wajan karatun su. Saboda kudin nan zai dan rage wa iyaye wasu waha-halun na makarantar yaran su. Su kuma yaran idan Gwamnati zata fara yi masu irin taimakon na makarantar nan, suma ba sai sun damu iyayen su da wasu bukatu na makarantar su ba, sai su biya duk abin da makaranta ta bukata gare su da wannan kudi na sukolashib.

Saboda haka ilimin bokon 'ya mace yana da muhimman fa'ida matuka a cikin al'umman mu, da kuma gidajan mu. Saboda haka nan nake kira ga Gwamnati da iyaye da babban murya da su hada hannu wajan kunkasa ilimi da kara farfado da murtaban ilimin boko na yara mata da kuma mata baki daya. Ta haka ne kasar nan zata kara yin fice a idon duniya mataban ta kuma ta karu saboda masu hikimar magana kan ce "mata idon gari ba ku ba gari in kunyi yawa gari ya baci"

Irin wannan kudi da Gwamnati ke bayarwa ga yara dake karatu a manyan makarantu, ya kama ta, ta fara bawa mata suma dake karaku kamar daga sakandare kafin ma su je ga zuwa manyan makarantu. Yin haka ga Gwamnati zai kara wa iyaye karfin gwaiwa kai hatta ma yaran dake zuwa makarantan za su kara kwazo da sa himma wajan karatun su. Saboda kudin nan zai dan rage wa iyaye wasu waha-halun na makarantar yaran su. Su kuma yaran idan Gwamnati zata fara yi masu irin taimakon na makarantar nan, suma ba sai sun damu iyayen su da wasu bukatu na makarantar su ba, sai su biya duk abin da makaranta ta bukata gare su da wannan kudi na sukolashib.

Saboda haka ilimin bokon 'ya mace yana da muhimman fa'ida matuka a cikin al'umman mu, da kuma gidajan mu. Saboda haka nan nake kira ga Gwamnati da iyaye da babban murya da su hada hannu wajan kunkasa ilimi da kara farfado da murtaban ilimin boko na yara mata da kuma mata baki daya. Ta haka ne kasar nan zata kara yin fice a idon duniya mataban ta kuma ta karu saboda masu hikimar magana kan ce "mata idon gari ba ku ba gari in kunyi yawa gari ya baci"